# Littafi mai Tsarki na yara
## Ke gabatar da

# Yakub mai yaudara



Wanda ya Rubuta: Edward Hughes

Mai Zane: M. Maillot; Lazarus
Alastair Paterson

Mai niyyan daukan nauyi: M. Kerr; Sarah S.

Fassarawa: Bible Society Nigeria

Wanda ya Wallafa: Bible for Children
www.M1914.org

©2024 Bible for Children, Inc.
Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan
har ba zaku sayar da shi.





Ko Allah ya taba aiko da jariri a iyalinka? Yaya kuka ji farin cikin? Ishaku da Rebekka dole ne sun kasance da cikakken farin ciki. Allah ya shirya ya ba su tagwaye.


Tagwayen suka yi ta kokawa da juna a cikin Rebekka. Lokacin da ta yi addu'a, sai Allah ya ce 'ya'yanta biyu za su jagorance al'ummai biyu – kuma karamin zai kasance mafi girma. Kullum babban yakan kasance mafi girma. Daga karshe, sai aka haifi jariran.
3
Tagwayen ba su yi kama da juna ba. Isuwa, wanda shi ne babban, yana da suma a jiki kuma ya girma ya zama gwanin mai farauta. Yakub kuma jikinsa babu suma kuma yana son aiki a gida. Baba Ishaku ya fi son Isuwa. Mama kuma tana son Yakub fiye da.
4
Wata rana, Isuwa ya ji yunwa. "Ba ni abinci," ya ce da Yakub. "Ka sayar mini hakkinka na 'ya'ya," in ji Yakub. Isuwa bai damu da alkawaran Allah wa yaro na farkon haifuwa ba. Sai suka yi yarjejeniya da juna. Yanzu, Yakub zai zama shugaban gidan bayan mutuwar mahaifinsu.
5
Wani dare, sai Allah ya yi magana da Ishaku. "Ni ne Allahn babanka, Ibrahim. Ina tare da kai. Zan albarkace zuriyarka." Ko da yake Ishaku ya yi wa Allah sujada, dansa Isuwa ya auri mata biyu daga Hitiyawa, mutanen da ba su damu da Allah ba.
6
Ishaku ya tsufa. "Ina roko ka kawo mini sabon nama." Ya ce wa Isuwa. "Sa'an nan zan sa maka albarka." Wannan albarka na musamman daga uba ne zuwa ga da na fari. Da sauri-sauri sai Isuwa ya fita farauta. Amma Rebekka ta ji maganarsu kuma tana so a sa wa Yakub ne albarkar.
7
Rebekka ta kulla wani shiri. Sa'ad da take shirya abincin da Ishaku yake so da sauri, Yakub ya saka rigunan Isuwa, sai ya saka rigunan dabbobi masu suma a hannayensa da wuyansa. Ishaku ba ya gani da kyau. Suna zato za su yaudare shi.
8


Sai Yakub ya kawo wa Ishaku abincin. “Ina jin ka kamar Yakub,” Ishaku ya ce, “amma hanayenka kamar na Isuwa ne.” Bayan da ya ci abincin, Ishaku ya sa masa albarka yayinda dan yana a durkushe a gabansa.
9


Nan da nan bayan da Yakub ya tafi, sai Isuwa ya zo wurin Ishaku. “Ga abincinka,” ya ce. Ishaku ya gane cewa an yaudare shi. “Ba zan iya canja albarkar ba,” ya yi ihu. Sai zuciyar Isuwa ya cika da kiyaya. Ya dauki ra’ayi zai kashe Yakub.
10


Rebekka ta ji barazanan Isuwa. “Ka tafi gidan kawunka,” ta ce wa Yakub, “sai dan’uwanka ya manta da abin da ka yi.” Ishaku ya yarda Yakub ya yi aure a iyalin mahaifiyarsa. Ta haka Yakub ya bar gida.
11


A daren nan, Yakub ya tsaya a wani wuri don ya yi barci, sai ya yi amfani da dutse don ya ajiye kansa. Watakila yana jin kadaici, ko kuma tsoro. Amma ba shi kadai ba ne. Allah ya yi magana da shi a mafarki mai ban mamaki.
12


“NI NE ALLAH NA KAKANINKA, IBRAHIM, DA ISHAKU. INA TARE DA KAI. ZAN BA KA WANNAN KASAR. TA WURIN IYALINKA DUKA IYALAI NA DUNIYA ZA SU SAMI ALBARKA.”
Bayan da Allah ya yi magana, Yakub ya farka. Yana jin tsoro.
13


Kawun Yakub Laban ya marabce shi. Yakub ya kaunace ‘yar’uwarsa na dangi mai suna Rahila sai ya yi wa Laban hidima na shekaru bakwai don ya aure ta.
Amma, a daren auren, Laban ya cuce Yakub.
14

"Wace nan Liyatu ce, ba Rahila ba," Yakub ya yi gunaguni. "Ka zambace ni." "Ai dole sai an aurar da 'ya ta fari kafin," Laban ya ce. "Yanzu sai ka aure Rahila ita ma kuma za ka yi mini hidima na shekaru bakwai kuma." Yakub ya yarda. Watakila ya tuna zamban da shi ma ya yi wa Ishaku da Isuwa.



15

Yakub ya haifi 'ya'ya goma sha daya. Sa'ad da shekaru suna karuwa, ya yi marmari ya mayar da iyalinsa zuwa Kan'ana. Iyayensa suna a wurin.



16

Haka ma Isuwa yana a wurin, kuma ya rantse cewa sai ya kashe shi. Lafiya ne ya koma? Wata rana Allah ya gaya masa ya koma. Yakub ya tattara iyalinsa da tumakinsa don ya kama hanya zuwa gida.



17

Babban tafiya kam. Isuwa ya zo don ya taraye Yakub tare da mutane dari hudu! Amma bai yi wa Yakub rauni ba. Ya ruga da gudu don ya marabci Yakub kuma ya rungume shi. Yakub da Isuwa suka zama abokai kuma, sa'an nan



Yakub ya dawo gida lafiya.

18

Yakub mai yaudara

Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

a na samu a

Farawa 25-33

"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130

19

KARSHE

6 60

20

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin**
**Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**